**Réseau National des Chambres d'Agriculture du Niger**

# Tirka daboobi

*Dr Soumaïla Abdourahamane (Responsable SVPP/ Fillingué), Issaka Boureima (CRA Dosso), / 19 mars 2019.*

Cibiyar kira domin samun bayyanai da shawarwari kan al'amuran noma da kiwo mai suna ISALAN da kungiyoyin RECA suka girka na samun kira lokaci zuwa lokaci kan yadda ya kamata ayi Tirka.

Manoman kasar Nijar maza da mata sun san tirka kuma sunayin tirkar bisashe tamkar sana'a. Saboda haka ya kamata su maida hankali kan shawarwarin da muka basu don su samu kinkawan sakamako, don kar suyi da na sani.

Da farko dai tirka,ita ce ka samu dabba ko ka sayi dabba mai kimanin shekaru biyu rago ko bunsuru), ka rinka cida ta don ta kasaita. To domin a samu sakamako mai kew, ya kamata a kiyaye wa'adin tirka,kada ya wuce watanni uku(3). Idan aka wuce wannan lokacin to maimakon a samu riba to faduwa za'ayi.




## Da wane lokaci ne ya kamata a shirya yin tirka?

Kahin ka sayi dabba daya ko biyu ko hiye da hakan don yin tirka ya kamata ka shirya; Kada ka shiga yin tirka ba tare da ka tanadi hanyoyin da zaka sama musu abinci ba; Ciyawa da dunsa,ka ajiye su guri mai kew; ka tanadi danyar ciyawa da harawar wake ko ta gujiya da sauran su sai a dandatse,a shanya cikin inuwa don su rike sindaran dake cikin su masu matukar unfani ga dabbobi.
Haka zalika dunsa da sauran tuwo suma a shanya su guri mai kew su bushe sosai don kar suyi hunhuna.
Ba a fara tirka sai an tanadi isashen abincin ,kenan ku sayi abincin dabbobi a lokacin

da yake da sauki(watoku tara abincin dabbobi lokacin da yake da sauki).

**Da wane lokaci ya kamata ayi tirka?**

Wasu kungiyoyi masu zaman kansu na tallafama mata a cikin sana'o'in da suke yin a yau da kulun; sai dai bai kamata ba a maida sana'ar tirka a lokacin sallar layya kadai; ya kamata masu tirka su samu lokuntan sayarwa biyu (2) ko unku(3) a cikin shekara, idan ba haka ba to yin tirka ba zai kasance sana'a ta yau da kulum ba;
Dabbobi masu maye,wanda suka samu tirka mai kew, nan da nan ake saye su kuma da kowane lokaci,sabili da haka mukaga ya kamata a wayema mata kai don su rinka tirke bisashen su koda yaushe kuma su maida hankali kan sauran kasuwanni ba sai lokacin layya kadai ba.

**Yaya ya kamata a zabi dabba?**

In dan bukatar layya ne,zaben dabbobi yahi maida hankali kan farare raguna ko fari da baki,ko fari da ja.
Shekarun rago kar su wuce biyu(2), saboda a lokacin nan ne yake cikin girma,indai yana samun kulawa mai kew,to saiyta girma nan da nan. Idan ba saboda bukatar layya ba,launin ragunan bai da wani mahimmanci.
Mutane sunhi maida hankali kan tirka raguna,jifa jifa ne su yin ta bunsunra.
A taikaice dai dabba mace wadda bata haihuwa,ana iya tirke ta.
Wakillai na cikin kasuwannin birane da kauyuka na kawo nasu taimakon a ko da yaushe gareku masu sayen dabbobi,don ku zabi dabba mai kew cewa da mai cikakan lahia da kuma wanda ya kamata a tirke , saboda akoye dabbobi masu lahia da wanda basuda ita,domin suna iya fahimtar dabba mai boyeyen ciwo saboda wasu dabbobi ciwon su ba a bayane ba ko kuma ta nada wata nakasa; kuyi unfani da shawarwarin su kahin ku sayi dabba.

**Mi yasa ake kebe dabbar da aka sayo,kuma yaya ne ake yi?**



Dabbar da aka sayo,ya kamata a kebe ta tsawon sati guda,abunda ake nuhi shine: kada a hada bakuwar dabbar da aka sayo daga waje da dabbobin gida don kare lahiyar dabbobin mu ko a gida ko kuma wa'idan ke zuwa wajan kiwo;kuma ta hakan ne za'a gano ko bakuwar dabbar bata dauke da wata cuta wanda zata iya sama sauran dabbobin.

Za'a kebe bakuwar dabbar tsawon sati 1 a cikin kewaye,wanan lokacin ya wadatas,kuma in dabbar mai ciwo ce,to za'a iya gane hakkan domin alamomin cutar zasu bayyana.

Bayan kun sayi dabbar to sai kuyi kokarin bata magugunan stustar ciki masu sinadirin ZOL kamar su albendazole,bolumisol da sauran su.
Wanda zaku iya samu a cikin ma'aikatun kiwo na gundumomi da na jaha(SVPP),da gidajan likitocin dabbobi masu zaman kansu da gidajan sayarda magugunan dabbobi.

Stutsostin  ciki na daya daga cikin abubuwan dake maida dabboni baya,lokacin kiwo ne dabbobi ke kamuwa dasu ko kuma a guraren shan ruwa.
Ku san da cewa yawan  neman ciyawar da dabbobi ke zuwa a cikin kasashen Africa na hadasa yaduwar tsutsotsin, don dabbobin ku su samu abincin ingantance ya kamata ku basu maganin tsutsa kai a kai.

Ya kamata asa tazarar sati daya bayan an bada maganin kashe  tsustar ciki saboda magani na kashe tsustar da ta konge ne baya kashe kwayayen,dalililin da yasa kenan ya kamata a maimaita bada maganin sati daya bayan nan farin don saboda a kashe kwayayan da zasu kinkinshe tsakanin wanan lokacin.
Bayan wannan za'a ba dabbar kwayoyin da zasu sa dabbar ta rinka cin abinci sosai,daga nan sai a mata alluran rigakahin cutitikan dabbobi kamar su cutar dake sa wuyan dabba ya juye, hancinta na zuba, ciwon kafafu, da kuma cutar da zata sa dabba ta kasa cin abinci, ta rame, da cutar da kesa kurage su fito ma dabbar cikin jiki kuma jikinta ya rinka zahi.
Mai dabba shine zai tanadi maganin kuma ya banbanta da shawshawar rigakahi gama gari da Gwamnati keyi.

**Yaya ne ake sa bisa tayi maye ?**

Da farko dai ya kamata a rinka ba dabba ciyawa kai a kai kahin a kai ga bata abu mai nauyi;
Ciyawar nasa dabbar ta samu  sauki wajan tika,abinci na biyu cewa da kamzo ko danyen tuwo da kunu na iya kawo ma dabbar mastala saboda nauyin shi, yana ma iya kashe dabbar in yayi yawa ;ya kamata a tanadi ruwa kai a kai, kuma ya kamata a samu gishiri,kanwa da makamantan su.

**Masu tirka ku kiyaye ?**




Tirka dabbobi na bukatar sanin asuwanni,abinci na kirki,zaben dabba da sanin yadda ya kamata a kula da ita ;
Musaman ma ku mata da kuka maida yin tirka tamkar sana'a kuma kuke jiran samun riba a lokuttan sallolin azumi dana layya;
To ku san da cewa akoye wasu lokuttan da kuke iya saida dabbobin ku da ba sai sallolin azumi dana layya ba;ku dai lura ,ita dai dabba mai maye bata konteye.

Idan kuna bukatar Karin bayani to sai ku tuntubi mashawartan nan na kugiyoyin **RECA** da **CRA** kan **92 24 24 24** (Orange) **- 89 97 97 74** (Airtel**) - 84 74 74 74** (Moov) **- 93 32 38 92** (Niger-telecom) ko kuma WhatsApp a kan **92 24 24 24.**

Wanan layoyin dai kungiyoyin **RECA** da **CRA** ne suka tanadar muku su don waye muku kai kan ayyukan ku na noman gandari dana tirka dabbobi.